**Manufofin Bambanci da Yaƙi da Bambanci na Sashen Nazarin Afirka**

1. Mun yarda cewa dukkanmu muna da yaƙinin cewa zamantakewa ko gata na tsari ko rashin gata, wanda ya shafi nau'ika daban-daban da wajen wariya, dangane da launin fata; yanayin jima'i; addini; naƙasa; ƙasashe; jinsi; matsayi cikin al'umma; shekaru; harsuna.
2. Sashen Nazarin Afirka yana da niyyar samar da zaman lafiya da kuma tabbatar da tattaunawa game da ƙasƙanci, bambancin launin fata da jinsi, kuma da samar da wurin karatu da yanayin aiki ga kowa da kowa, a kowane lokaci.
3. Muna goyon bayan cuɗanya da haɗin kan dukkan al'umma ba tare da la'akari da launin fatarsu ba; yanayin jima'i; addini; naƙasa; ƙasashe; jinsi; matsayin zamantakewa; shekaru; harsuna.
4. Mun amince da Muhimmin Jawabin da Majalisar Ɗinkin Duniya ta bayyana game da Hakkokin 'Yan Adam, musamman da wajen kiyaye 'yancin ra'ayi da bayyana ra'ayi (duba sashi na 19).
5. Muna fatan magance dukkan ƙanana da manyan lamuran da suka shafi wariyar launin fata a tsakaninmu, kuma in ya zama dole a haɗa da ƙwararru da membobin wasu ƙungiyoyi masu haɗin gwiwa.
6. Don magance wariya muna sauƙaƙa matakai ta wajen bayanan jama'a, tattaunawa, bita, da horo ga masu horarwa.
7. An kafa wani tsari na gaskiya don magance shari'o'in nuna wariya masu zuwa tare da tsarin ƙorafi da nasihohi, jarrabawa, da sakamako, waɗanda aka zaɓa a kan kowane lamari.
8. Muna ba da tabbacin rashin bayyana dukkan mai ƙorafi a kan wariya in ya so haka.
9. Mun tabbatar da cewa wannan manufar tana samuwa a bainar jama'a kuma ana iya amfani da ita a zaman tushe don iƙirarin wariya.
10. Ana samun wannan manufar cikin yarukan: Swahili, Bambara, IsiZulu, Hausa, Larabci, Jamusanci, Ingilishi, da Faransanci.